Kashi na 1
Littafin
Zabura

# Yabo da Sujada

Darasi na 1



### A KAN ME AKE MAGANA?

A ƙarshen darasin nan ya kamata ɗalibai su:

- san yadda za su ji dadin yabon Allah ta hanyoyin dabam-dabam.
- san ba laifi ba ne idan nan mori kayan dabam-dabam.
- nuna kauna da bangirma ga Allah lokacin sujada da yabo.

### ME NAKE BUKATA?

- Littafi Mai Tsarki
- Littafin rubutu da Biro
- Shirya mutane biyu don gabatarwa.

AYYUKAN SHAKATAWA! MINTI 15

## GANGUNA DA RAWA??

Mutane biyu su kwaikwayi Audu da Yakubu da wannan tattaunawa.

**Yakubu:** Littafi ya bayyana yadda mutane suka yi amfani da kayan ki]e-ki]e iri-iri domin ]aukakar Allah.

**Audu:** Yana da kyau mu ]aukaka Allah da dukan zuciyarmu. Raira kananan wa}o}i na tsawo lokaci da buga ganguna da }arfi sukan hanna mu tunani mai kyau.

**Yakubu:** Amma kuma yabo da ]aukaka suna tafiya tare. Jin da]in wa}o}i da rawa suna shafan ko ina a jikinmu. Dole ne mu mika zukatanmu da tunaninmu da nufinmu cikin }auna da yabon Allah.

**Audu:** A she muna }aunar Allah kuma muna girmama shi ke nan idan muna hayaniya a gabansa? Gangunan suna tuna mini rawan gargarjiya, kai ma ka san abin da wannan yake nufi!

**Yakubu:** Idan mun yi yabo da addu'a, Allah zai ji da]in kararrakin da suna zuwa daga zukatanmu.

**Audu:** A tunanina, ina gani zai ji da]i idan muna girmama juna ta yadda yabonmu zai kai gare shi ta hayar da ta dace. Wannan ne abin da Bulus ya yi magana a kai a 1kor. 14:40.

Ka sa membobi su yi tunani akan ra'ayoyi dabam-dabam da a ka bayana, amma kada a bata lokaci mai yawa a nan.

NAZARIN L.M.T MINTI 25

## Murna da Bangirma

**Karanta zabura 33:1-11**
**[aukaka mai girma**

1. Ta yaya marubucin Zabura ya ce za mu ]aukaka Allah (aya 1-3)?
2. Wa]anne abubuwa aka ambata a aya 2?
   a) wa]anne kayan muzika suka yi kama da irin na wannan zamani?
   b) Ta yaya aka ce za mu more su?
   c) Ina ma'anar wannan gare mu a yau?
3. Fa]i dalilan da aka bayar a aya 4-11na ]aukaka Allah.
   Lissafa su a kalkashin wa]annan kawuna
   a) Halin Allah
   b) Aikinsa na halitta
   c) Ayyukansa tsakanin al'umma
4. Wa]anne kalmomi biyu aka mora a aya 8 da suka bayyana halinmu game da Allah lokacin da muna yabon sa?
   Wa]anne kalmomi za ka mora a yau saboda bayyana halinmu wajen ]aukaka Allah?

**Karanta Zabura 33:12-22**
**Kaunarsa madawwami.**

5. Wa]anne albarku ne ke ga wa]anda Allah shi ne Ubangijinsu?
6. Yaya ya kamata halinmu ya zama ga Allah (aya 18-21)?
   Ta wace hanya za mu sa zuciya ga Allah yayin da muke jiransa (aya 19-20)

# Allahnmu yana mulki

K**aranta Zabura 47:1-9**
**Raira wa}o}in yabo ga Allah.**

7. Me muke nunawa yayin da muke tafa hannu muna raira wa}a (aya 1)?

8. Wa]anne abubuwa biyu ake so daga mutanen Allah a wannan Zabura? Ko ana wa]annan abubuwa a lokacin sujadarmu kullayaumi?

9. Fa]i hanyoyin da marubucin Zabura ya bayana cewa Ubangiji shi ne sarki a wannan Zabura.
   Ta wace hanya matsayinsa na ]aukaka ya zama abam da na sauran sarakuna (aya 8, 9b)?

10. **Menene tunaninka?**

- **Ziyartar Gwamna.**
  Ta yaya za ka nuna bangirma da muryarka da abin da za ka yi? Me zai yi idan ka abin da za ka yi? Me zai yi idan a yi masa? Don me? Sawa?

- **Kai da Allah kadai.**
  Ta kaka zan bayyana masa }aunata da dogara ga ayyukansa na ban mamaki? Dole ne in fa]a masa da babban murya? Ta yaya zan tabbatar masa da gaskiya }aunata zuwa gare shi?

- **Ma'anar Sujada.**
  Dubi Romawa 12:1-2.
  Me ya fa]a game da halin sujada a rayuwarka? Ta yaya aikinka ko nazarinka ke nuna halin yin sujada ga Allah.



# Sujada mai am'ana

Kowane memba ya za~i ]aya daga cikin kungiyoyin nan uku.

[auki minti 10 ka shirya yadda za ka yi sujada.

Bayan minti 10, kowace }ungiya ta yi sujada ta yadda suka shirya.

**Kungiya ta 1**
Yi yabo cikin natsuwa da rawa cikin hankali. Yi addu'a cikin kankanuwar murya. Karanta wasu ayoyi daga Zabura.

**Kungiya ta 2**
Za~i wakar yabo. Shirya domin buga tafi da rawa. Mori kayan kida.

**Kungiya ta 3**
Za ku makaranta ko ma'aikata. Nuna yadda za ka yi makaranta ko aiki ta hanyar da ka yi wa Allah sujada.

**Addu'a:**

⇒ Gode wa Allah saboda zarafin da ya ba ka don ka ]aukaka shi saboda dukan ayyukan da ya yi maka.

⇒ Ro}i Ruhu Mai Tsarki ya nuna maka yadda za ka yi wa Allah sujada da dukan zuciyarka da kowane bangare na rayuwarka.

⇒ Ro}i Allah ya taimako ka don ka iya bayyana wa wasu kirista ma'anar sujada ga Allah cikin murna da bangirma.

## AIKIN GIDA NA WANNAN MAKO:

**Rana a 1**
**Karanta**
Zabura 33:1-5

**Rana ta 2**
Yi bimbini a kan
Zabura 47:2-3

**Rana ta 3**
Haddacewa
Zabura 47:8

**Rana ta 4**
Karanta
Zabura 33:13-21

**Rana ta 5**
Yi tunani a kan
Zabura 33:6-12

**Rana 6**
Haddacewa
Zabura 33:22;47:7